# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Tuntuɓar juna tsakanin addinai: Haɗin kan mutanen Sodangi
## Kashi na biyar: Muhawara mai zafi

Wanda ya rubuta: Romie Singh
Wanda ya tace: Katrin Ogunsade, Naïma Guira
Wanda ya fassara: Ɗanlami Bala Gwammaja

**'Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Shugabar makaranta (Madam Titi): | 'yar shekara 48 |
| Tafida: | ɗan shekara 17 |
| Dauda: | ɗan shekara 17 |
| Ɗanjuma: | ɗan shekara 16 |
| Layla: | 'yar shekara 16 |
| Saima: | 'yar shekara 16 |
| Baban Tafida: | ɗan shekara 50 |
| Fada Bana: | ɗan shekara 49 |

**MAI GABATARWA:**
Masu sauraronmu, barkanmu da sake kasancewa da ku a cikin wani sabon shirin na “Ji Ka Karu” mai taken “Haɗin kan mutanen Sodangi”, wanda aka shirya a kan yadda addini da siyasa suka zama tarnaƙi a tsakanin wasu al’ummomi guda biyu da kuma wasu gidaje biyu. Yau ne ranar da kowa ya ƙagara ta zo, wato ranar ƙaddamar da Kungiyar Muhawara ta Kwalejin Zumunta.

**Fitowa ta 1: A Kwalejin Zumunta**
Shugabar makaranta, Tafida

**SHUGABAR MAKARANTA:** Ɗalibai, ina yi muku barka da asuba, kuma barkanmu da saduwa a taronmu na safe.

**KOWA DA KOWA:** Barka da asuba, Malama.

**SHUGABAR MAKARANTA:** Kamar yanda kuka sani ne wannan makaranta tamu ta samo sunanta ne daga daɗaɗɗiyar aƙida ta Afirka, wato zumunta. Ita wannan kalma ta zumunta ta ta’allaƙa a kan tausayawa, da cuɗanya, da kuma kula da tsare mutuncin juna. Domin na tunatar da mu wannan aƙida tamu, da haƙuri da girmama juna, bari mu yi wata addu’a. Ba zan faɗa muku ko wannan addu’a ta ’yan Afirka ce ba, ko ta Amurkawa ce, ko ta Musulmai ce, ko kuma ta Kiristoci ce ba. Muhimmin abin shi ne addu’ar ta yi tasiri a zukatanku. Bari mu yi addu’ar!

**ƊALIBAI da SHUGABAR MAKARANTA:**
*Ya Ruhi mai girma,*
*Wanda yake raya dukkan duniya, ka karɓi addu’ata.*
*Ina buƙatar taimako da hikima daga gare ka.*

*Ina neman wannan taimako ne ba don na fi kowa ba,*
*sai don na yaƙi babban maƙiyina, wato zuciyata.*
*Ka ba ni ikon kusantarka ko da yaushe.*
*Ina mai tsarki kuma mai kyakkyawar zuciya,*
*yadda zai zama ko da rayuwata ta shuɗe,*
*ruhina zai sadu da kai ba tare da tozarta ba.*

**SHUGABAR MAKARANTA:** To yaya, wannan addu'ar ta yi tasiri a zukatanku? … Wannan addu'ar wani ɗan asalin ƙasar Amurka ne, mai suna Chief Yellow Lark, ya tsara ta a shekarar 1887. Abu ne mai muhimmanci mu dage wajen ƙulla zumunta musamman ma a rayuwa irin ta yau. Ya kamata mu dunƙule mu zama ɗaya a matsayinmu na 'yan Adam maimakon a matsayinmu na masu addini iri ɗaya. Don haka dokar nan da ta hana sa wata alama da za ta nuna irin addinin da mutum yake bi tana nan daram. A bisa wannan tsarin, wannan doka ta shafi irin tufafin da mutum zai saka. Sai dai ɗalibanmu Musulmi sun faɗa mana cewa lalle ne su su sa riguna masu dogon hannu da dogon wando, sannan sai sun rufe kansu in har za su yi wani wasa na motsa jiki a wajen makaranta, inda sauran jama'a na iya ganinsu. In ko ba haka ba sun ce su ba za su yi wani wasa ba. Wannan ya sa dole ne mu yi ƙoƙarin nemo mafita. Saboda haka zan gabatar da wannan batu, don a tattauna a kan irin kayan wasan da ya dace su yi amfani da shi a taronmu na Hukumar Makaranta na gaba. Bugu da ƙari, yau ne da yamma da misalin ƙarfe uku za mu ƙaddamar da sabuwar Kungiyar Muhawara ta wannan makaranta. Ina yi muku fatan alheri, sai an jima.

**ƊALIBAI:** Sai an jima, Malama.

**MAI BA DA LABARI:**

To, ko a wane irin hali Tafida zai sami kansa a ciki a wannan rana? Yana jin ma Layla ko ganinsa ba ta yi ba domin ya shiga wannan Kungiya ta Muhawara ne don kawai ya sami kusanci da ita. Amma ita ba ta ma san yana yi ba.

**Fitowa ta 2: A Kungiyar Muhawara**

Dauda, Layla, Ɗanjuma, Tafida, Saima

**DAUDA:** To, ya isa haka nan. Don Allah a saurara! Barkanku da rana. Gaskiya na ji daɗin ganin kun sami halartar taron ƙaddamar da wannan ƙungiya tamu ta muhawara. Layla ce shugabar taron namu, kuma ita ce za ta fara tofa albarkacin bakinta.

**LAYLA:** Na gode, Dauda. Da farko ina miƙa godiyarmu ga shugabar wannan makaranta, saboda damar da ta ba mu na yin amfani da wannan aji har na tsawon minti 45. A tsari irin wannan, muna buƙatar kafa dokoki don mu ji daɗin tafiyar da wannan ƙungiyar. Don haka kuna iya ba da shawararku a kai, ni kuma zan rubuta!

**ƊANJUMA:** Halartar harkokin ƙungiya ba fashi!

**TAFIDA:** A dinga ba kowa dama yana faɗar ra'ayinsa!

**SAIMA:** A dinga kashe waya!

**LAYLA:** Haka ne. Don Allah duk wanda zai yi magana ya ɗaga hannu, kuma kada a katse wa mutum hanzari in yana magana. Batun da yawancinku suka zaɓa shi ne auren mace fiye da ɗaya. Kafin

mu fara, bari na yi wata tambaya: Me kuka sani game da auren mace fiye da ɗaya? To, Saima, me za ki ce?

**SAIMA:** Wata al'ada ce da ake yi a al'ummar da maza suke danne haƙƙin mata. Al'ada ce wadda ta ba maza dama su auri mace sama da ɗaya. Sai dai su matan ba a ba su dama su auri namiji sama da ɗaya ba. Kamar yadda yake a Kundin Haƙƙoƙin Ɗan Adam na Majalisar Ɗinkin Duniya kamata ya yi a ce daidai muke.

**ƊANJUMA:** Daidai da wa? Kina nufin ku dinga yin abin da maza suke yi? Wannan shirme ne.

**SAIMA:** Gaskiyarka Ɗanjuma! Amma in haka ne me ya sa aka ba maza dama su auri mace sama da ɗaya?

**ƊANJUMA:** Ai haka al'adar take, Saima. Tun shekaru aru-aru da suka wuce maza suke auren mace sama da ɗaya, wataƙila ko don su haifi 'ya'ya da yawa.

**LAYLA:** Don Allah duk wanda yake son ya yi magana ya ɗaga hannunsa. Umm... Tafida kana da ta cewa ne?

**TAFIDA:** Ni a fahimtata auren mace sama da ɗaya wani tsarin rayuwa ne ga dattijai, don su tara yaran da za su kula da su in sun tsufa.

**ƊANJUMA:** Haka ne fa! Haka ma in manoma ne iyayen, ka ga za su sami waɗanda za su taimaka musu wajen nomansu da kuma kiwo. Kuma ba ka da cewa don me?

**SAIMA:** Kai! Amma ina da ja! Kar ku manta fa wannan ƙungiya ce ta muhawara!

**ƊALIBAI:** Haka ne kuwa! Gaskiya ne!

**LAYLA:** Don Allah a saurara! Ina so na tambaye ku: Me ya haɗa ba wa mata 'yanci daidai da maza da auren mace fiye da ɗaya?

**SAIMA:** Ba wata alaƙa!

**LAYLA:** To. To, ya isa haka! Wannan haka yake, akwai ƙarin bayani kuma?

**ƊANJUMA:** Ai Musulmi na auren mace sama da ɗaya.

**LAYLA:** A'a, ni babana bai yi ba.

**SAIMA:** Ni ma babana bai yi ba.

**ƊANJUMA:** To, shi ke nan. Wasu daga cikin Musulmi su ne suke auren mace sama da ɗaya.

**SAIMA:** Da wasu Kiristoci ma. Ko'ina ma ana yi, a Amurka da ƙasashen Turai, ba wai a Afirka kawai ba. Su kawai abin da suke kiran irin wannan al'ada shi ne, mutum ya ajiye dadiro, ko su ce yana harka.

**DAUDA:** Don Allah ku yi shiru! Ya isa haka nan! A yi shiru! A matsayina na mai shiga tsakani a wannan muhawara, ina so na nuna muku cewa akwai bambanci tsakanin auren mace sama da

ɗaya, da kuma mutum ya ajiye dadiro ko a ce yana yin harka. Sam ba ɗaya suke ba. Duk mutumin da yake da mata biyu a Afirka, to sai da ya nemi izinin ta farkon tukuna kafin ya ƙara ta biyu. Kuma dole ne ya ɗauki nauyinta ya kuma gina mata gida. Wannan ya bambanta da mutum ya ajiye dadiro ko ya dinga yin harka a waje. Ajiye dadiro ko yin harka a waje, abu ne wanda mai yi ba ya so a sani. Amma shi auren mace sama da ɗaya yana da bambanci domin abu ne mai tsari.

**SAIMA:** E lalle kuwa! Tsarin namiji ba!

**LAYLA:** Don Allah a saurara! A tsarin muhawara ana so a sami ra'ayi guda biyu mabambanta. Don haka ga tambaya: Shin an yarda cewa al'adar nan ta 'yan Afirka ta auren mace sama da ɗaya, karɓaɓɓiya ce a tsarin al'adun Afirka na wannan zamanin?

**SAIMA:** A'a sam! Ba a yarda da ita ba! Abin da wannan ya nuna shi ne su maza ba za su iya jure takaicin ganin matarsu ta ƙara wani mijin ba, amma ita matar dole ne ta jure. Don Allah ku dubi abin da idon basira. Yaya mace za ta ji a ce ga mijinta da wata matar?

**MAI BA DA LABARI:**

Bayan an tashi daga muhawarar, sai Tafida ya ɗan tsaya don ya yi magana da Layla, amma hakan ba ta samu ba saboda suna ta hira ita da Dauda. Don haka, kawai sai ya yanke shawarar ya je gidansu ya jira ta, don kuwa ya san ba da daɗewa ba za ta koma, amma ba ta dawo ɗin ba. Maimakon ya gan ta, sai ɗan'uwan nan nata ya gani ya sunƙe wani abu kamar kwalba. Sai kawai ya haƙura ya koma gida. Yana buɗe ƙofar shiga gida sai ya sami babansa cikin wani yanayi na nishaɗi.

**Fitowa ta 3: A gidan su Tafida**

Baban Tafida, Tafida

**BABAN TAFIDA:** … E, canza kanun labarin. … Yauwa, ka mai da shi "Wata coci ta ƙone". … Yauwa, to sai an jima. … Ah kai! Gaskiya Tafida, ina cikin nishaɗi!

**TAFIDA:** To me ya sa? Me ya faru Baba?

**BABAN TAFIDA:** Yaro, kana wasa da baban nan naka! Ni fa na amsa sunana. Ai na sha gabansu! Muryar Sodangi ce jaridar da za ta fara fasa ƙwai gobe da safe, kuma za mu buga sunayen waɗanda suka haddasa gobarar.

**TAFIDA:** Wace gobara?

**BABAN TAFIDA:** Wadda ta tashi a Cocin St. Thomas mana. Duba ka gani! Yaranmu ne suka ɗauki hoton wannan yaron kafin motar ɗaukar marasa lafiya ta tafi da shi.

**TAFIDA:** Wane hoton? Mu gani?

**BABAN TAFIDA:** Ai ka gane shi ko? To ni ma na gane shi! Ba abin da zai hana na faɗa wa Fada Bana wanda ya ƙona masa coci.

**MAI BA DA LABARI:**

Daga wannan magana, sai baban Tafida ya ɗauki waya ya kira kawun Dauda, wato Fada Bana.

**Fitowa ta 4: A gidan su Dauda**

Fada Bana, Dauda

**FADA BANA:** Me ka ce? … To, na ji. Ka kyauta da ka faɗa min.

**DAUDA:** Mene ne Kawu?

**FADA BANA:** Ka ga irinta ko Dauda! Na ja kunnenka a kan ka daina shiga harkar yarinyar nan Layla in kun tashi daga makaranta. Ko kana son ka san me ya sa? Da kai nake! To yanzun nan wani yaro ya ƙone mana coci a bakin titi. Kana so ka san ko waye? To ƙanenta ne, yaron nan Hassan Umar! Kai kuma kana nan kana yi wa 'yar'uwarsa kwarkwasa.

**DAUDA:** Haba dai! Hassan ɗin?

**FADA BANA:** Malam Magaji, mutumin da ya amsa sunansa, babban edita na Muryar Sodangi ne ya faɗa min, yana kuma da hotonsa. Allah wadaran zuriyar su Umaru ɗin nan. Ba za mu taɓa ƙyale su ba. Kai kuma ka saurare ni da kyau, daga yau ba kai ba wannan Musulmar yarinyar in an tashi daga makaranta. Ka ji ko Dauda?

**MAI GABATARWA:**

Yau kuma a nan muke dasa aya a cikin shirin namu na "Ji Ka Karu" a kan "Haɗin kan mutanen Sodangi". Kona cocin Fada Bana ta ƙara hura wutar zaman doya da man ja tsakanin Musulmi da Kiristoci a garin Sodangi. Sai kuma a biyo mu a shiri na gaba domin jin yadda za ta kaya. In kuna buƙatar sake sauraron wannan shirin ko aiko da tsokaci, kuna iya tuntuɓarmu ta adireshinmu na yanar gizo, wato www.dw-world.de/lbe.